ï»¿RIJIYA GABA DUBU 1
Saurayin gudu yake iya karfinsa acikin dajin domin ya ceci rayuwarsa,yana gudu yana waigen bayansa cikin tsananin tsoro,amma baya ganin komai kuma baya jin sautin komai face na masifaffun karnukan dake biye dashi.
Su dai wadan nan karnuka sun kai guda saba in da doriya kuma sun kasance jibga jibga tamkar ba karnuka bane kai kace kurayene sabo da girmansu da kwarjininsu gami da ban tsoro,musamman aka kiwata wadan nan karnukan kuma aka basu horo na musamman domin suyi gadin babban kurkuku na birnin Kisra.
A tarihin birnin na kisra tunda aka gina kurkukun tsawon shekaru arba in ba ataba samun fursuna da ya taba guduwa daga cikin sa ba sabo da karfin tsaron da ke cikinsa sai wannan saurayi wanda ake kira IMHAL IBN IMZANU,sabo da tsananin karfin gudun Imhal ne ya baiwa karnukan tazara ta kimanin taku sittin amma sabo da nacin karnukan da mugun horon da suka samu sai gashi sun fara hango shi,nan fa suka kara kaimi,nan fa Imhal ya kara kaimin gudunsa alokacin da ya waigo ya hango su yaci gaba da falfala azababben gudu ta cikin kwazazzabai da sarkakiya,sabo da karfin gudun ma har tashi sama yake yana tsallake duwatsu da karyayyun bishiyoyin da suka fadi kasa.
Shi dai Imhal gudun kawai yake yi acikin dajin amma baisan inda yake dosa ba,sabo da baisan ma a inda yake ba bare ma yasan hanyar da ya kamata yabi, a duk sanda ya tuno da bakar wahalar da ya sha kafin ya sami nasarar guduwa daga kurkukun sai ya kara kaimin gudun nasa yana mai ayyanawa a ransa da dai a kamasa a raye a mai dashi cikin kurkukun gwara a sami gawarsa sabo da azabar da take cikin kurkukun ta wuce tunanin mai tunani.
Asalin Imhal bin Imzanu mutumin birnin misira ne kuma shi ba dan kowa bane kuma bai aikata laifin komai ba,mahaifinsa wani makiyayi ne mai kiwon dabbobi a daji,don haka rayuwar Imhal gaba daya a cikin daji take,sai dai a karshen kowane sati ranar Lahadi sukan shiga cikin gari suyi dan siye-siyen su sannan su koma daji inda suka gina bukkarsu.
Imhal ya taso da Jarumtaka juriya da iya farauta,sanan komai yawan dabbobi idan ya tafi kiwo dasu yana iya sarrafa su.
Lokacin da Imhal ya fara girma ya cika shekaru goma sha shida ne ya tambayi mahaifinsa tsoho Imzanu yace ya kai Abbana me yasa baka taba bani labarin mahaifiyata ba?ban santa ba kuma bansan yanda akayi ta mutu ba kullum sai kace dani kawai mutuwa tayi,kayi sani cewa yanzu ni ba yaro bane karami na mallaki hankalin kaina yakamata ka sanar dani gaskiyar al amari,koda tsoho Imzanu yaji wannan batu sai hankalinsa ya dugunzuma ainun yayi shiru yana mai sunkui da kansa kasa,kawai sai idanunsa suka ciko da kwalla hawaye ya fara zubowa kas, a sannan ne ya dago kai ya dubi Imhal yace yakai dana kasani yau ka tambayeni wani sirri wanda dama nayi alkawarin bazan sanar dakai ba sai bayan ka mallaki hankalinka,don kada hankalinka ya dugunzuma kwakwalwarka ta kasa daukar al amarin, koda imzanu yazo nan a zancensa sai ya sake yin shiru kamar bazai ia cewa komai ba,da kyar ya ake dago kai ya dubi Imhal muryarsa na rawa yace ka gafarceni yakai dana bisa abinda zaka ji daga bakina yanzu domin zakayi matukar mamaki kuma zai iya girgiza ka,maganar gaskiya ita ce ni ba mahaifinka bane na jini,koda jin wannan batu sai zuciyar Imhal ta buga da karfi,nan take idanunsa suka kada sukayi jawur,bai san sanda hawaye ya zubo masa ba yace yanzu idan ba kaine mahifina ba to wanene? Bansan kowa ba a rayuwata sai dai kai kadai,kaine kasan cina da shana tundaga kuruciyata har izuwa yanzu,me yasa uban nawa ya gujeni ya barni a wajanka cikin daji

inda babu jin dadi da tsaro?lallai kuwa ashe babu soyayya tsakani na da uban nawa tunda bai damu da rayuwata ba.

TO JAMA'A KUYI MIN AFUWA SAI NA HUTA ZAN CIGABA.

RIJIYA GABA DUBU 1 Cigaba1

Koda Imhal yazo nan a zancensa sai tsoho ya zubar da hawaye sannan yace Ni kaina bansan waye mahaifinka ba,ka saurara dakyau kaji labarin da zan baka yanzu,wata kila idan kaji labarin zuciyarka tayi sanyi ka rungumi kaddara a bisa halin da ka tsinci kanka a ciki.

Wata rana da safe na fito kiwo acikin dajin nan ina kada dabbobi na sai kawai na hango wasu mutane bisa keken doki sanye da bakaken tufafi kuma sun rufe fuskokinsu su biyu sun nufi bakin wani katon rami mai zurfi da fadin gaske,cikin hanzari na kada dabbobina izuwa cikin duhuwar bishiyoyi nima na sami wuri na buya,dama wadannan mutane basu ganni ba,ina nan labe cikin duhuwa sai naga wadannan mutane sun fiddo gawar wata mace daga cikin keken dokin sun cillata cikin wannan ramin,kawai sai suka shiga cikin keken dokinsu da sauri suka fice daga cikin dajin gaba daya,sai da na tabbatar da cewa sunyi nisa da tafiya kuma babu alamar cewa zasu dawo sannan na ruga izuwa bakin wannan ramin na leka cikinsa kawai sai naga ashe wata kyakkyawar mace ce aka yanka ta har a sannan jini na bulbulowa daga cikin makogwaronta kuma tana dauke da tsohon juna biyu,nan take naji na kamu da tsananin tausayinta,don haka sai na yanke shawarar na shiga cikin ramin na dauko gawar wannan mata domin na suturta ta sosai na haka kabari mai kyau na binne ta,idan ma na barta acikin ramin zata rube ne warinta ya dameni tunda ramin yana kusa da inda bukkata take,nan fa na fara tunanin dabarar da zanyi na iya shiga cikin wannan rami har na iya dauko gawar,sai da nayi tunani na tsawon 'yan dakiku sannan dabara ta fado mini,kawai sai na ruga da gudu izuwa cikin bukkata,na dauko igiya mai tsawo sannan na dawo bakin ramin,na daura igiyar a jikin wata bishiya na wurgata cikin ramin sannan na kama igiyar ina binta ina shiga ramin,sannu a hankali na isa kasan ramin,koda naje kan gawar na duba ta sai naga ashe da ranta bata mutu ba domin numfashinta na fita kadan-kadan,cikin gaggawa na sunkuci wannan mace na goya ta a bayana na daureta tamau,na sake kama igiyar nayi iya kokarina na fito daga cikin ramin goye da matar a baya na,hankalina a dugunzume,sauri nake kawai na jarraba ceto rayuwarta,ina fita daga cikin ramin na ruga da ita izuwa cikin bukkata,na shimfide ta a kasa sannan nayi sauri na dauko allura da zarin dinke fata na dinke raunin wuyanta sannan na shafa magani akan raunin,A sannan ne na kara hancina a dai dai hancin matar don naji ko tana yin numfashi,amma sai naji shiru alamar babu rai a jikinta,nan fa bakin ciki ya lullube ni naji kamar na fashe da kuka sabo da takaici,gashi nasaa wahalar dauko ta daga cikin wannan ramin mai zurfi har ma tafin hannuwana sun dade saboda kama igiya,cikin sanyin jiki na mike na sunkuya da nufin daukar gawar na fita da ita waje inda zan binne ta,kawai sai naji tayi tari,numfashinta ya dawo,nan take murna ta kamani na ruga na dauko wani ruwan magani na dura mata a baki dakyar tasha mukurwa uku,jin kadan sai idanunta suka bude dakyar,koda tayi arba dani sai naga ta firgita ta yunkura zata tashi amma sai na danne kafadunta na hana ta tashi,matar ta budi baki da nufin tayi magana sai ta kasa,kawai sai naga tana dariya,wani lokacin kuma sai ta hade fuska ta kama kuka tana fisge-fisge,nan fa na gane lallai wannan mata ta samu tabin hankali,al'amarin da yayi matukar bakanta raina kenan domin naso ace ta iya yin magana acikin hankalinta,domin na tambayeta ko ita wacece da kuma wadannan mutane da suka kawo ta dajin acikin keken doki a matsayin gawa,abinda zuciyata ta aiyana min shine in ma basu bane to sun san wanda

ya kasheta,kuma akwai wani boyayyen al'amari akan kisan nata,daga wannan rana naci gaba da jinyar wannan mata har tsawon kwana ashirin da daya,A tsawon wadannan kwanaki kullum a kwance take kuma koda tayi yunkurin mikewa zaune sai ta kasa sabo da raunin da yake makogwaronta,haka kuma bata taba yin magana ba sai fisge-fisge da dariya irinta mahaukata,abinci kuwa sai dai na dura mata abaki tana ci tana kuka sabo da ciwo,da yake naga tana dauke da juna biyu sai na dinga yawan bata madarar shanu gami da abincin da yake gina jiki domin abinda ke cikinta ya samu cikakkiyar lafiya,a kwana a tashi har wannan mata ta shafe wata uku cur a wajena,a sannan ne raunin makogwaronta ya warke sumul har ya zamana cewa tana iya magana sosai,amma a koda yaushe babu magana ta hankali da nutsuwa a tare da ita sai maganganu irin na mahaukata,nayi iya kokarina akan ta gayamin ko ita wacece,daga inda take da kuma yadda akayi ta shiga wannan hali sai tayi ta kyalkyala mini dariya,ganin hakane yasa tausayinta ya karu a zuciyata,sau bakwai ina nemo masana ilimin maganin mahaukata,wato likitocin mahaukata suna zuwa su dubata kuma su bata magani,amma duk a banza lafiya taki samuwa,sau tari matar takan sulale ta nausa cikin daji bansani ba,sai nasha wahalar nemota,bisa wannan dalilin ne ma duk sanda zan fita kiwo ko farauta sai na tafi tare da ita,wato na daina barinta a gida.

TO JAMA'A AYIMIN AFUWA SAI NA HUTA ZAN CI GABA

RIJIYA GABA DUBU1 CIGABA 2

Lokacin da cikinta ya tsufa sai tafiya da ita kiwo ko farauta ya gagara,don haka nima sai na hakura da zuwa ko ina,na tanadi abincina da na dabbobi na mai yawa wanda zai kai tsawon kwana arba in,Ai kuwa adaren kwana na talatin da bakwai nakuda ta kama wannan mata acikin tsakiyar dare.Al'amarin da yai matukar dugunzuma hankalina kenan tunda babu halin in ruga cikin gari in nemo ungozoma,Da yake na taba shiga irin wannan hali da nake tare da matata wacce ta rasu a wajen haihuwa abinda ta haifa ma yazo a mace,sai na shiga taimakon wannan mata,nine na yankewa jaririn cibiya,na wanke shi sannan na kimtsa mahaifiyar tasa,matar taci gaba da rainon jaririnta tana shayar dashi ni kuma ina cigaba da fita farauta da kiwona ina barinsu a gida,har tsawon shekara daya da wata bakwai muna tare sannan yaron ya fara tafiya da kafafunsa.

Kwatsam wata rana naje kiwo na dawo sai na nemi wannan mata sama da kasa na rasa,kuma ga dannan ta bar shi acikin bukka a zaune shi kadai yana ta tsala kuka,cikin dimaucewa na dauki yaron na gaya shi a bayana sannan na bazama neman wannan mata wacce ko sunanta ban saniba bare na dinga kwalla mata kira,Abu kamar wasa sai da na shekara daya da wata tara ina nemanta amma ko alamunta ban gani ba acikin wannan daji.A tsawon wannan lokacin ni nake kula da wannan yaro da ta haifa dare da rana,ya zama cewa na shaku dashi ainun shima haka

.Kwatsam wata rana da yammaci ina wasa da yaron a kofar bukkata kawai sai na hango wannan mata daga can nesa ta durfafo bukkata,cikin alamun tsananin mamaki na mike tsaye na zuba mata idanu,matar ta rame matuka,kuma duk rigar jikinta ta yayyage,sannan tayi baki sabo da wahala da kazanta,koda ta iso daf dani ta dubeni sai ta fashe da kuka ta durkusa kasa bisa gwiwoyinta  tana mai neman gafarata tamkar mai cikakken hankali,nan take naji na kamu da tsananin tausayinta don haka sai na kama kafadunta na tasheta tsaye kuma na rungumeta a kirjina a karon farko tun haduwa ta da ita,ita kuma sai ta kankame ni ta da da fashewa da kuka,kawai sai na janye jikina daga nata na dubeta nace me yasa kika gudu kika barmu?shin

kin manta ne cewa kin bar danki a hannu na?koda jin haka sai matar ta dubi dan nata  ta girgiza kai tace ai ni kananin yaro na bar maka bai kai wanan girma ba,da jin haka sai nayi dariya nace to ai kullum mutum dada girma yake har yanzu baki gaya min inda kika tafi ba kika barmu,Matar ta bushe da dariya sannan ta hade fuska tace shan iska na tafi na sake dawowa.Cikin tsananin damuwa nace yau shekara hudu kenan muna tare baki taba gaya min sunanki ba kuma baki gaya min sunan garinku ba bare nasan asalinki da danginki shin bakya tausayin wannan yaron da kika haifa ne?Koda jin wannan tambaya sai matar ta sake bushewa da dariya tace bansan kaina ba kuma bansan kowa ba sai kai,tana gama fadin haka ta juya ta shige cikin bukka taje ta kwanta ta kama bacci,tun daga wannan rana muka ci gaba da zama tare,amma ko kadan wannan da nata bai dameta ba,kuma bata yi masa komai sai dai ni nayi masa,wani lokaci sai naga kamar hankalinta ya dawo tana magana a nutse,amma da zarar na fara tambayarta asalinta da garinsu sai ta birkice ta koma hauka.
Wata biyu da kwana uku mukayi tare ranar kwana na ukun ne matar ta wayi gari da tsananin rashin lafiya wadda bansan sanadinta ba,cikin rudewa na shiga hada mata magunguna iri-iri ina bata tana sha amma duk a banza tamkar kara mata ciwon akeyi,kawai sai naga idanunta sun fara lumshewa kuma numfashinta na sarkewa,Al amarin da ya dugunzuma hankalina kenan na fara zubar da hawaye,na shiga yi mata tambayoyi akan ta sanar dani asalinta,matar na kokarin bude baki tayi magana amma sai ta kasa,nan take jikinta ya sandare,idanunta suka kafe ta daina motsi.koda naga haka sai na rungumeta na fara kuka,ganin ina kuka ne dannata wannan yaro dan shekara kusan hudu ya rugo izuwa kaina shima ya fashe da kuka.Hakika wanan rana nayi kuka mai yawa sabo da shakuwar da nayi da matar nan sai da nayi kwana ashirin da daya bana iya cin abinci sosai,amma koda yaushe hankalina yana kan wannan yaron ina kula da lafiyarsa sosai.
Koda tsoho Imzanu yazo nan a zancensa sai Imhal ya tari numfashinsa suka dubi juna a lokacin da kowannensu yake zubar da hawaye yace yakai Abbana na gane cewa wannan yaro da mahaukaciya ta haifa ba wani bane face ni dinnan,tabbas yanzu na tabbatar da cewa ni marayane wanda bashi da uwa bashi da uba kuma wanda baisan asalinsa ba,koda Imhal yazo nan  zancensa sai tsoho Imzanu ya rungumesa suka fashe da kuka tare,can sai Imhal ya janye jikinsa suka fuskanci juna ya dubi Imzanu yace Bazan taba yarda bani d uba ba amma ni kai na sani a matsayin ubana,ina son nayi maka wata tambaya guda daya menene dalilin da yasa kake kirana da suna IMHAL?
TO JAMA'A NIMA NA GAJI IDAN NA HUTA ZAN CIGABA DAGA MAI SON NISHADANTAR DAKU COMBATANT33
RIJIYA GABA DUBU1>CIGABA3
Koda jin wannan tambaya sai hawaye ya zubowa tsoho Imzanu yace Abinda yasa nasa maka suna Imhal shine a iya zama na da mahaifiyarka har ta mutu ban taba jin ta ambaci sunan wani mahaluki ba face IMHAL,A kullum duk sanda za taci abinci sai naji tana kiran sunansa tana cewa yazo suci abincin tare,abinda na fahimta shine,koma wanene wannan Imhal din lallai ya kasance babban masoyi a gareta,zai iya kasancewa mijinta ne ko dan uwanta ne ko mahaifinta,Abu na biyu da nake zargi shine,duk yadda akayi mahaifiyarka ta fito daga babban gida domin a ranar da na tsince ta acikin wannan katon ramin mai zurfi sutturar dake jikinta mai matukar tsada ce,babu mai sanya irinta face sarakai da manyan attajirai,babban bakin cikina shine babu wata shaida a tare da mahaifiyarka wadda zata iya sawa a gano asalinta,koda tsoho

Imzanu yazo nan a zancensa sai suka sake rungume juna,daga can sai Imhal ya dubi tsoho Imzanu yace,Lallai zan rike sunana a zuciyata da bakina,lallai wata rana wannan suna zai taimakeni na gano asalina.
Tun daga wannan rana Imhal da tsoho Imzanu suka cigaba da rayuwarsu acikin daji kamar yadda suka saba,amma sai ya zamana cewa kullum sai Imhal ya shiga cikin garin Kisra kuma duk inda yaje si ya tambayi mai suna Imhal,idan aka tambayeshi wane Imhal yake nema sai ya kasa bayani domin baisan wata inkiya ba ta Imhal din da yake nema,hakane yasa suka dinga yiwa Imhal dariya suna cewa dashi Bagidaje mutumin daji,saboda ganin yanayin shigarsa ta makiyaya.
Wata rana Imhal yazo giftawa ta kofar gidan sarkin kisra akayi sa a kuwa a lokacin sarki ya fito daga cikin gidan sarautar zai fita rangadi kwatsam sai yayi arba da sarki,Abinka da wanda baisan yadda ka idar sarauta take ba sai kawai ya kurawa sarki idanu,maimakon ya zube kasa gabansa ya kwashi gaisuwa,ai kuwa sai dakarun sarki suka afkawa Imhal da duka har suka kai shi kasa,cikin fushi ya yunkura ya watsar dasu duka duk da cewar sunkai su ashirin,nan take shima ya rufesu da duka,duk wanda yayi wa naushi daya sai ya baje a kasa sumamme,koda ganin haka sai ragowar dakarun sarki suka zare takubbansu sukayi caa akan Imhal zasu sassara shi,amma sai sarki ya daka musu tsawa suka saurara,nan take sarkin kisra ya sauko daga kan dokinsa yazo daf da Imhal yadda har suna iya jin numfashin juna,sannan ya dubeshi cikin murmushi yace,A duniya babu abinda yake birgeni sama da jarumtaka,tabbas na yarda kai jarumi ne amma ina son na gwada jarumtaka ta akan taka,nasan baka san koni waye ba to nine Sarkin garin nan,koda jin haka sai Imhal ya zube kasa bisa gwiwoyinsa yana mai sunkui da kansa kasa yace ka gafarceni ya shugabana,kasan cewa ni rayuwata gaba daya cikin daji nayi ta,sau daya a sati muke shigowa cikin garinnan,yau ne ranar farko da na fara ganinka a rayuwata,ya shugabana kayi min afuwa domin bazan iya fada da kai ba,Koda jin wannan batun sai sarki ya bushe da dariya ,lokaci guda kuma ya hade rai ya dubi Imhal cikin nutsuwa yace,ya kai wannan saurayi ma abocin jarumtaka kayi sani cewa nahiyar nan gaba daya babu wani jarumi ko mayaki mai karfi da iya yaki kamata,yau shekara talatin kenan ina gwagwarmaya da gumurzu kuma sau arba in da uku ina lashe GASAR JARUMTAKA a kasashe arba in da uku dake cikin wannan nahiya tamu ko sau daya ba a taba samun jarumin da ya lakuci jikina ba bare ya kaini kasa,naga jarumtakar jarumai da yawa a rayuwata,amma ban taba ganin jarumi mai zafin nama da karfin naushi kamarka ba,ina da tabbacin cewa idan muka fafata sai na sami nasara akan ka duk da cewar na yaba da karfinka,ka sani cewa kana da zabi guda biyu kodai ka yakeni ko kuma yanzun nan nasa tagobi na sare maka kai,koda jin wannan batu sai hankalin Imhal ya dugunzuma ya mike tsaye cikin sanyin jiki,abu na farko da ya fado masa a rai shine,Ai bai kamata ya mutu yanzu ba har sai ya gano asalinsa,koda gama aiyana hakan acikin zuciyarsa sai ya mikawa wani badakare hannu yace bani tagobinka,ba tare da gardama ba kuwa ya mikawa Imhal tagobinsa ya karba,koda ganin haka sai murna ta kama sarki,shima ya zare tagobinsa,a lokacinne dakaru suka buda suka yi musu da ira aka sa su a tsakiya,nan fa sarki da Imhal suka fara zagaya juna suna kallo-kallo.
TO JAMA'A KUYI MIN AFUWA IDAN NA HUTA ZAN CI GABA DAGA MAI SON NISHADANTAR DAKU IBRAHIM S COMBATANT
RIJIYA GABA DUBU1 CIGABA 4
Lokaci guda kowannensu ya daga tagobinsa sama suka ruga izuwa kan juna,suka runguntsume

da azababben yaki ya zamana suna kaiwa juna sara da suka cikin tsananin zafin nama,juriya da bajinta ta ban al'ajabi,sai da suka shafe sa a guda suna wannan bakin artabun amma dayansu bai samu nasarar koda kwarzanar mutum daya ba,Al'amarin da ya fusata sarki kenan kuma ya cika da tsananin mamakin yadda akayi wannan mutumin dajin ya samu gagarumin horon yaki haka,nan take sarki ya canza salon yaki,ya dinga tsalle-tsalle da kwance-kwance,kawai sai yaga Imhal ya iya duk irin abinda yake yi tamkar tare aka koya musu yaki babu wani banbanci,koda ganin haka sai sarki ya ja da baya taku biyar,shima Imhal sai yayi hakan amma shi taku uku yayi,duk su biyun suka kurawa juna idanu na tsawon yan dakiku kadan,kawai sai sarki ya rugo da gudu izuwa kansa,shima sai ya ruga gareshi,kafin su hadu sai kowannensu ya daka wawan tsalle sama ya kai hari cikin mugun nufi,Acikin tsananin zafin nama kowannensu ya kaucewa harin takubbansu suka sari iska,amma kafin su duro kasa sun gwarawa juna fuska,ai kuwa sai hancin kowannensu ya fashe,a saman sai suka sake kaiwa juna hari,sai sarki ya sami nasarar yankar Imhal a saman cibiyarsa,Shi kuma ya sami nasarar yankar sarki a gefen wuyansa,kowannensu jini yayi tsartuwa daga jikinsa suka rikito kasa a matukar galabaice,A guje Dakaru suka ruga aka baiwa Sarki rawani ya daure wuyansa da jini,take likitan Sarki yayi masa magani,Kawai sai Dakaru suka ruga izuwa kan Imhal wanda yake kwance a kasa ya dafe raunin don tsaida jini zasu halaka shi,Sarki ya daka musu tsawa suka fasa,kawai sai sarki ya dubi likitansa yace Idan ka gama dani kaje kayiwa wannan saurayin magani,Cikin gaggawa kuwa likita ya gama yiwa sarki magani sannan yaje yayiwa Imhal,Sa ar da Sarki da Imhal sukayi raunikan basuyi zurfi ba a jikin su,Tunda Likitan ya fara yiwa sarki magani sai zuciyar Sarki ta fara tafarfasa kamar zata kone saboda tsananin bakin ciki da takaici bisa ganin yadda a yau wannan bakon saurayi ya karya alkadarinsa na jarumin dake rike da KAMBUN JARUMTAKA na nahiyar gaba daya,Bayan angama yiwa Imhal magani ya mike tsaye sai yazo gaban Sarki ya risina yayi godiya,Sarki ya dube shi cikin yake yace Tabbas ka cika jarumi abin kwatance amma ka saurari ranar da zamu sake haduwa a filin gasar JARUMTAKA wacce za ayi a birnin MISIRA nan da cikar wata uku,ko kana so ko baka so sai ka shiga wannan gasa kuma ina tabbatar maka da cewar sai na sami nasara akan ka na kasheka murus har Lahira,yin hakane kadai zai sa na huce bisa takaici da bakin cikin da ka jefani a ciki,Koda ya gama fadin hakan sai Sarkin Kisra ya dubi wani babban Badakare nasa yayi masa rada a kunne sannan ya juya ya kama dokinsa ya hau ya kada linzaminsa yayi gaba,sauran dakarun gaba daya suka rufa masa baya.Shi kuwa jarumi Imhal sai ya tsaya cak yabi sarkin kisra da kallo cikin tsananin mamaki,Imhal ya tambayi kansa cikin zuciyarsa yace WAI SHIN MENENE YAYI ZAFI HAKA,HAR DA SARKI YACE ZAI KASHENI MURUS HAR LAHIRA ALHALIN MA BASU TABA GANIN JUNA BA SAI YAU?AKAN WANE DALILI ZAI TSANANTA GABA A TSAKANINMU HAKA?koda Imhal ya kasa baiwa kansa amsa sai ya juya ya falfala da gudu ya nufi hanyar da zata kaishi daji.

To jama'a ayimin afuwa zan cigaba idan na huta daga mai son nishadantar daku IBRAHIM S COMBATANT

RIJIYA GABA DUBU 1 CIGABA 5

Imhal ya ci gaba da gudu har sai da ya iso dajin da bukkarsu take,yana cikin gudu ne ya hango tsoho Imzanu ya goyo jakarsa ta tafiya yana dogara sanda ya baro bukkar acan baya,cikin kaduwa da matukar mamaki Imhal ya karasa wajen Imzanu da gudu ya tareshi yana mai rike kafadunsa ya dube shi yace Ya kai abbana lafiya kuwa?ina zaka je naga ka dauko jakarka ka

nufi hanyar cikin gari?Koda tsoho Imzanu yaga Imhal a tsaye gabansa sai fuskarsa ta fadada da murmushin farin ciki,har ya budi baki zai ce wani abu sai idanunsa suka kai kan raunin dake kan kasan cibiyar Imhal,cikin firgici Imzanu ya dube shi yace yaya akayi ka samu wannan raunin?koda jin wannan tambayar sai Imhal ya kwashe labarin duk abinda ya faru tsakaninsa da sarki Kisra ya zayyana masa ba tare da boye masa komai ba,koda jin wannan labarin sai hankalin tsoho Imzanu ya dugunzuma ainun har idanunsa ya ciko da kwallah ya dubi Imhal yace ya kai dana ina so ka sani cewa kamar yadda ka kasance maraya a garin nan haka nima nake,iyayena da kakannina duk sun mutu,matata ta mutu tare da dan da ta haifa kamar yadda na baka labari,A halin yanzu bani da kowa face kai wane irin hali kake tsammanin zan shiga idan na rasaka?ina mai tabbatar maka da cewa idan har ka halacci gasar jarumtakar da za ayi nan da cikar wata uku a birnin Misira sai ka rasa rayuwarka domin tabbas sai sarkin garinnan ya kashe ka,domin zai je yayi gagarumin shiri ne yayi amfani da karfin sihirin tsafi wanda dole sai ya samu nasara akan ka,A halin yanzu bamu da wani zabi wanda ya wuce mu sulale mu bar Nahiyar nan gaba daya,indai muka isa wata nahiyar daban shikenan mun tsira daga sharrin sarkin kisra,duk inda muka tsinci kanmu sai mu fara sabuwar rayuwa,duk da cewa ni tsufa ya kamani ina da sauran buri guda daya a duniya,wannan burin ba na komai bane face nason ganin aurenka,koda tsoho Imzanu yazo nan a zancensa sai Imhal ya rungume shi suka fashe da kuka tare tsawon yan dakiku suna manne da juna sai daga can Imhal ya janye jikinsa daga cikin nasa ya dube shi yace Ya kai Abbana kayi sani bazan yi maka gardama ba bisa wannan shawara da kazo min da ita,sabo da nasan cewa ni bansan abinda kasani ba,domin duk wanda ya riga ka kwana dole ya riga ka tashi,yanzu sai mu koma bukkarmu mu debo kayanmu gaba daya,Imzanu ya gyada kai yace Ai na debo mana dukkan kudadenmu idan mun shiga cikin gari mayi guzuri,cikin alamun tsananin damuwa Imhal ya dubi imzanu a lokacin da idanunsa suka ciko da kwallah yace Haba ya kai Abbana ko ba komai na koma da baya ka nuna inda ka binne mahaifiya ta nayi mata bankwana tunda rabona da ita tun ina kankani,koda jin wannan batu sai hawaye ya zubowa Imzanu ya dubi Imhal yace ka gafarceni ya kai dana hakika naso nayi babban kuskure,zo muje na nuna maka kabarin mahifiyarka,ko da gama fadin haka sai tsoho Imzanu ya juya da baya suka koma izuwa can gaban bukkarsa suka cigaba da nausawa cikin daji suna bin wata hanya mai sarkakiya da yawa wacce shi kanshi Imhal a iya tasowar shi acikin daji bai taba sanin akwai wannan hanya ba,kawai sai tsintar kansa yayi acikin wadansu dogayen bishiyoyi masu manyan ganyaye wadan da suka sa dajin gaba daya yayi duhu,bisa dole suka kunna wuta a jikin itace don haska hanya,Imzanu ya cigaba da yiwa Imhal jagora sai gasu a bakin kofar wani kogon dutse mai girman gaske,da isowarsu bakin kofar kogon sai Imzanu ya haska cikin kogon yaga lafiyarsa sannan ya juyo ya dubi Imhal ya mika masa wutar itacen yace acikin wannan kogon na binne mahaifiyarka,ka shiga ciki zaka ga kabarinta sai kayi mata bankwana ni kam bazan iya sake kallon kabarin ta ba domin idan na gan shi zan tuno baya,kuma hakan zai iya jefani cikin mugun hali,cikin matukar sanyin jiki Imhal ya karbi wutar icen sannan uya kunna kai cikin kogon dutsen yana shiga kuwa ya hango kabarin na mahaifiyarsa,kai tsaye ya tukari inda kabarin yake da isarsa gaban kabarin sai ya durkusa a gabansa ya kifa kansa akan kabarin sannan ya fashe da matsanancin kuka tsawon yan dakiku yana cikin wannan hali sannan ya dago ya kurawa kabarin idanu yace YAKE MAHAIFIYATA SABO DAME ZAKI TAFI KI BARNI LKACIN DA NAFI BUKATARKI FIYE DA KOMAI?ME YASA KIKA TAFI BAKI FADI KO WAYE UBANA BA?SHIN HAKA KIKE SO RAYUWATA TA KARE

ACIKIN KADAICI, MARAICI GAMI DA TAKAICI KAMAR YADDA TAKI TA KARE?WANENE IMHAL?SUNAN DA KIKE AMBATA AKO DA YAUSHE?IDAN HAR BAZA KI IYA BUDAR BAKI KI GAYA MIKI AMSAR TAMBAYOYINA BA YANZU ZAN KASANCE MAI SAURARON FATALWARKI KODA ACIKN BARCINA,BAZAN TABA SAMUN SUKUNI DA KWANCIYAR HANKALI BA A RAYUWATA HAR SAI NA GANO ASALINA.
Koda gama fadin hakan sai Imhal ya sake kifa fuskarsa akan kabarin ya dada fashewa da kuka bakin ciki.
To jama a ayimin afuwa idan na huta zanci gaba
RIJIYA GABA DUBU 1 CIGABA 6
Sai da ya jima yana kukan sannan ya mike tsaye ya fice daga cikin kogon dutsen yana waigen kabarin yana zubar da hawaye,har ya isa bakin kofar kogon zai fita sai ya waigo ya dubi kabarin yace Yake ummata nayi miki alkawarin zan rayu acikin wannan duniya komai RINTSI DA TSANANI har izuwa lokacin da zan gano asalina na dawo har nan na sanar dake,koda gama fadin haka sai ya juya ya fice daga cikin kogon yana fitowa ya iske tsoho Imzanu a zaune ya kishingida da jikin kogon har ya fara bacci sabo da gajiyar yaar tafiyar da yayi,motsin takun sawun Imhal ne yasa ya farka daga baccin cikin yanayin damuwa,Imzanu ya dubi Imhal yace yakai dana kayi sani cewa na gaji ainun kuma gashi tsufa yana tabani ina ganin cewa yanzu bazan iya takawa da kafafuna ba yanzu sai dai mubarwa gobe da safe amma yin hakan yana da hadari,domin ina ji a jikina cewar sarki zai iya turowa a kamaka domin ya tsareka a kurkukunsa,don kada ka gudu kabar garin,kafin tsoho Imzanu ya gama rufe bakinsa sai suka jiyo sautin takun sawu daga can nesa,alamar takun sawu ne ta mutane da yawa kuma inda suke aka durfafo,koda jin haka sai Imhal yayi wuf ya suri tsoho Imzanu ya goyashi a bayan sa ya daure shi tamau,sannan ya ruga izuwa kan wata bishiya mai tsawon tsiya wacce can karshenta ganyayene manya manya masu duhuwa,kamar kadangare na hawa bango haka Imhal ya dinga hawa kan bishiyar da gudu kai kace ba sama yake hawa ba,cikin dakiku kadan ya isa karshen bishiyar yayi lambo akan wani reashe,shi kansa Imhal idan ya leko kasa baya iya jiyo motsin komai sabo da nisa,A dai dai wannan lokaci ne dakaru acikin bakaken kaya kimanin su dubu suka iso dai dai kofar kogon dutsen da gudu,dukkanninsu suna rike da tagobi tsirara kuma sun rufe fuskokinsu,koda tsoho Imzanu ya hango wadannan dakaru sai ya sai zuciyarsa ta buga da karfin gaske ya firgita ainun ya fara kokarin tuno da wani al amari wanda ya faru a shekarun baya,amma sai kwakwalwar tasa ta kasa tuno komai.Dakarun masu bakaken tufafi na isowa suka tsaya cirko cirko suna kallo kallo da waige waige,nan dai shugabansu ya rarraba su izuwa gabar da yamma kudu da arewa,suka bazama neman inda su Imhal suke,har cikin kogon dutsen inda kabarin mahaifiyar Imhal yake sai da suka shiga.A dai dai wannan lokacine Imhal yayi kundunbala ya sallamo kasa daga kan doguwar bishiyar,karar dirar kafafunsa kasa ne yasa dakarun suka farga suka baro inda suke da gudu,amma kafin su iso inda suka bari tuni Imhal ya falfala da azababben gudu goye da tsoho Imzanu,Wohoho!kafa me naci ban bakiba?idan zan ta tarar da muje mu sai abinda hali yayi,duk tsananin gudu irin na Imhal sai gashi wadannan dakaru suna rufa masa baya har ma suna nema su cimmasa amma sun kasa,koda dakaru suka ga an shafe dakiku masu yawa sun kasa cimma Imhal duk da tsananin nacinsu gami da horon da suka samu na juriya sai suka fara zaro kibiya suna danawa akan baka suna harbawa Imhal,Imhal na cikin gudu sai yaji kibiyoyi suna wucewa ta samansa da gefensa,har ma sai da wata kibiya ta karci gefen kunnensa jini yayi tsartuwa,al amarin da

yayi matukar girgiza hankalinsa kenan ya kara karfin gudunsa,amma abinda ya kara tayar masa da hankali shine,tunowa da tsoho Imzanu wanda ke goye a bayansa wanda ako da yaushe bisa tsautsayi kibiya zata iya zuwa ta soke shi,koda ya aiyana hakan sai yasa hannayensa ya juyo da tsoho Imzanu daga bayansa ya dawo dashi gabansa ya ci gaba da falfala gudun da haka,kaico!Tsautsayi ba a yi masa barci!Imhal na cikin wannan azababben gudu ne kibiya tazo ta soke shi a duga duginsa na kafar hagu take kibiyar ta ta nutse ta hudo waje,Imhal ya kwarara uban ihu sakamakon tsananin zafi da zugin da yaji,yayi taga taga kamar zai kife kasa amma sai ya yunkura cikin zafin nama da tsananin juriya ya take kafar a haka tana zubar da jini yaci gaba da gudu.Naci damben kuturu!koda dakarun nan suka ga Imhal yaki faduwa kasa yaci gaba da gudu duk da cewar kibiyar ta soke shi a kafa sai suma suka ci gaba da falfala gudu suka dada zubo masa ruwan kibbau ba sassauci,Har Imhal ya iso daf da kafar cikin gari dakarun basu cimmasa ba kuma babu wata kibiya data soke shi amma fa yana jin mugun zugi acikin kafarsa tamkar ya sare kafar da hannunsa ya yar da ita.koda dakaru suka ga an iso cikin gari sai suka samu lokuna suka shiga suka buya suka sauya tufafin jikinsu suka sa irin na mutanen gari suka bude fuskokinsu,sannan suka rarrabu suna masu dada ci gaba da farautar Imhal.Imhal na shigowa cikin  birnin kisra goye da Imzanu sai ya fara sarewa yana jan kafa da kyar,cikin hanzari ya doki kofar wani gida dake rufe da hannunsa guda, take kofar ta balle ya kunna kai ciki ya yunkura zai kwance Imzanu daga jikinsa sai yaga ashe ya suma sakamakon wata kibiya data soke shi a gefen wuyansa,cikin tsananin dimaucewa Imhal ya sauke Imzanu kasa ya wangame baki zai rusa ihu don a zatonsa Imzanu ya mutune,sai kawai yaga wata tsaleliyar mata ta rugo da gudu daka can cikin gidan ta dube shi tana mai yi masa inkiyar yayi shiru.

TO ZAN HUTA ANAN SAI KUNSAKE JINA

RIJIYA GABA DUBU1 CIGABA7

Sai da tazo daf da shi sannan tayi masa rada a kunne tace tsohonka bai mutu ba,zan iya ceto rayuwarsa ni likita ce,bari nayi sauri naje na batar da shaidar da zata sa a gane ka shigo nan,maza ka shigar da tsohon can cikin dakina ka kwantar dashi kada ka taba shi,tana gama fadin haka sai ta dauki wani tsumma ta ruga waje,cikin sauri Tsaleliyar matar taje ta goge duk jinin kafarsa,daya zuzzuba a kofar gidan,sannan ta sake rugawa izuwa cikin gidan ta mai da kofa ta saka sakata.Faruwar haka ke da wuya sai ga wadannan dakaru da suka biyo Imhal sun iso wajen da gudu,gaba dayansu sai suka tsaya suna yin duru duru suna waige waige da hange hange,suna jiran karasowar shugabansu domin ya basu umarni bisa abinda za suyi

Al'amarin Imhal kuwa,lokacin da ya kinkimi tsoho Imzanu ya shige dashi izuwa dakin  wannan tsaleliyar mata a dimauce sai ya shimfide shi akan wani babban teburi na katako,a sannan ne ya dubi ko ina a cikin dakin nan take ya gamsu cewa daki ne na likita,don babu komai acikinsa face tarkacen kayan likitoci,kawai sai ga matar ta shigo cikin dakin da gudu,ko kallon Imhal batayi ba ta ruga izuwa kan tsoho Imzanu ta shiga yi masa aiki,nan take ta cire kibiyar dake wuyan nasa,ta zuba wani garin magani akan raunin nan take jini ya daina zuba,duk wannan abu da take Imhal yana tsaye a gefe daya ya zuba mata idanu kawai cikin tsananin mamaki,domin bai san dalilin da yasa ta taimake shi ba alhalin gashi ma yayi mata laifi ya karya mata kofar gida da karfin tsiya,kuma gashi bata taba ganin shi ba sai yau,Bayan gama shudewar dakiku dari da ashirin da gama yiwa Imzanu magani sai ya farfado ya bude idanunsa,koda ganin haka sai farin ciki ya lullube Imhal ya kama yiwa matar godiya,A dai dai wannan lokaci ne suka ji ana kwankwaso kofar gidan da karfi,Al'amarin da ya  tayar da hankalin Imhal ya yunkura zai zare

tagobinsa,sai matar tayi masa nuni da kada ya zare tagobin,ta dube shi tace ka bani yardarka ina mai tabbatar maka da cewa komai dadewa zaka dawo ka iske mahaifinka a cikin koshin lafiya,maza kayi sallama da tsohon naka zan nuna maka hanyar da zaka bi ka fice daga cikin gidan nan ba tare da wani ya ganka ba,cikin tsananin mamaki Imhal ya dubeta yace wacece ke kuma sabo dame kika ce ci rayuwarmu nida wannan tsohon nawa?matar tayi murmushi mai taushi ga Imhal tace Ni na sanku fiye da shekaru bakwai baya,kune baku san ni ba,kuma na dade ina bibiyarku a duk sanda kuka shigo garinnan,tana gama fadin haka ne suka ji anci gaba da buga kofar gidan da karfin gaske,A guje matar ta kama hannun Imhal ta jashi izuwa cikin wani dakin daban yana waigen tsoho Imzanu yana hawaye,shima Imzanu ya bishi da kallo yana zubar da hawaye,domin duk su biyun sun san cewa abu ne mai wuyar gaske idan har zasu sake saduwa da junansu,da shiga su Imhal cikin wannan daki na biyu sai sukayi arba da wata rijiya a bude wacce ta ciko da ruwa har baki,kai sai matar ta dube shi tace kayi nitso izuwa can kasan rijiyar zaka samu hanya wadda zata kaika har izuwa kogon Ishmal dake can bayan gari,daga nan sai ka nausa daji kayi kokarin ficewa daga nahiyar nan gaba daya,kada ka kuskura ka dawo garinnan sai bayan anyi gasar Jarumta a birnin misra koda gama fadin haka sai matar ta juya da baya,cikin sauri Imhal ya ruko hannunta,ta waigo ta dube shi cikin mamaki yace mata mene sunanki? Matar yai murmushi tace mishi sunana ZUMAIRA IBINI IMHAL.Koda jin wannan suna sai idanun Imhal suka zazzaro ya kasa sakin hannunta kuma a sannan ne suka ji anbugo kofar gidan da karfi ta fadi rikica gaba daya,koda ganin haka sai matar tasa kafarta ta doki kirjin imhal ya fada da baya cikin rijiyar,kawai sai ya nutse izuwa karkashinta,cikin hanzari matar ta juya ta koma baya da gudu.Tana isowa falonta ta iske tsoho Imzanu zaune akan teburin cin abinci yana shan ruwan Inibi kuma har ya sauya tufafin jikinsa,kuma ya sauya kamanninsa domin ya shafe gemunsa da sajensa da shuni kamar bashi ba,wadansu karti kimanin su arba'in na tsaye a gabansa daya daga cikinsu nayi masa tambayoyi,kawai sai Zumaira ta dakawa kartin tsawa ta dube su tace,su waye ku akan wane dalili zaku karya mana kofar gidanmu ku shigo?koda jin haka sai Dakarun suka waigo izuwa kan zumaira suna muzurai kamar saci babu har sun zare takubbansu zasu afka mata sai daya daga cikinsu ya daga musu hannu suka dakata sannan ya matsa daf da Zumaira ya dubeta a fusace yace muna neman wani saurayi da wani tsoho mai furfura a gemunsa ki gaya mana gaskiya idan sun ahigo gidannan kun boye su domin idan kuka yi mana karya kuma mukayi bincike muka gansu sai mun kasheku,koda jin haka sai Muzaira tayi guntun murmushi tace ai sai ku duba ku gani,nan take katti suka bzama ko ina amma basu ga kowa ba,sannan suka fice daga gidan gaba daya. To jama'a kuyi min afuwa zan cigaba idan na huta

RIJIYA GABA DUBU1 CIGABA 8

Muzaira ta dubi tsoho Imzanu kawai sai taji ya fashe da kuka,al amarin da ya karya zuciyarta kenan ta kamu da tsananin tausayinsa don haka sai ta dube shi tace Ya kai Imzanu ka kasance mai gaskiya da juriya acikin duk irin yanayin da ka tsinci kanka aciki,koda jin haka sai Imzanu ya dago kai ya dubeta cikin mamaki yace Ya akai kika san sunana?yayin da muzaira taji wannan tambaya,sai nan take idanunta suka ciko da kwallah sannan ta dubi Imzanu tace Mahaukaciyar da kayi jinya acikin daji har ta haifi wannan saurayi da kuke tare yayata ce uwarmu daya ubanmu daya,kuma ita ce babba a wajen mahifinmu wanda shine sarkin kisra na da,kafin azzalumin sarkinmu na yanzu ya kashe shi ya hau kan karagar mulkinsa.Gaba daya zuri armu sai da sarki GURZALU ya kashe su,nice kadai nayi saura,nima albarkacin karfin sihirin tsafin da

nake dashine yasa na tsira da rayuwata,Ba wani abune yasa yar uwata ta haukace ba face a gabab idanunta aka kashe mijinta Imhal aka yi masa yankan rago,sannan aka yanka iyayenmu da dukkan zuri'armu,tana ganin wannan al'amari ne ta haukace nan take,amma duk da haka sai da aka yi mata yankan rago akasa dakaru sukayi badda kama suka dauki gawarta suka kai daji suka yar,Abinda yasa aka dauki gawarta aka kaita daji shine,Ramin da aka haka aka saka gawar mijinta da ta sauran zuri'armu ya cika.Duk abinda ya faru da yar'uwata Shulaira na gani a madubin tsafina,kuma duk naga irin dawiniyar da ka sha da ita shi yasa yanzu na taimake ku na kubutar da Imhal,ina mai tabbatar maka da cewa Imhal ya kubuta daga sharrin sarki Gurzalu domin zai fice daga cikin garin nan gaba daya ta cikin wata rijiya dake cikin gidannan.koda Muzaira tazo nan a zancenta sai tsoho Imzanu ya cika da tsananin mamaki gami da tsananin bakin ciki,daga can kuma sai ya dubi Muzaira cikin alamun damuwa yace Ke kuwa mai yasa tun yar'uwarki na raye a wajena a daji baki ziyarce ta ba,kuma me yasa yanzu baki gayawa Imhal cewar ke kanwar mahaifitarsa bace?Muzaira tayi ajiyar zuciya tace Ai ina fita daga cikin garinnan sihirin tsafina zai karye sarki Gurzalu ya gano inda nake ya turo a kashe ni,dalilin da yasa ban sanar da Imhal ni uwace a garshiba shine,idan na gaya masa bazai tafi ba yanzu kuma idan yaki tafiya ni dashi halaka zamuyi,koda jin haka sai hankalin tsoho Imzanu ya tashi fiye da ko yaushe ya rasa abinda ke masa dadi a duniya.
Lokacin da Imhal ya nutse izuwa cikin karkashin wannan rijiya ya isa can kasanta sai ya kama laluben hanya,nan da nan ya fara fita daga hayyacinsa sakamakon rashin numfashi,amma cikin sa a sai yaga wani kifi yas shigo cikin rijiyar ta cikin wata kofa,cikin sauri ya kunna kai cikin kofar sai ya ganshi akarkashin wani katon kogi,ciin sauri ya taso sama domin ya shaki numfashi,aikuwa yana dagowa sama yaji an gabza masa duka da kulki a fuska,take jini yayi feshi daga cikin bakinsa da hancinsa nan take ya baje a saman ruwa sumamme.
To jama'a ayimin afuwa wlh cajina ya kare zan cibaga ba da dadewa ba
RIJIYA GABA DUBU1 CIGABA9
Sa'adda Imhal ya farfado sai ya tsinci kansa acikin wani matsatstsen daki kwance a kas,gefensa ga wani garjejen saurayi a zaune ya kura masa idanu,cikin dimaucewa da mamaki imhal ya mike zaune zumbur ya karewa dakin kallo tsaf,sannan ya dubi garjejen katon saurayin dake gabansa yace,Ina ne nan?Yaya akayi nazo nan?koda jin wannan tambaya sai katon ya bushe da dariyar mugunta,maimakon ya baiwa Imhal amsar tambayarsa sai ya mike tsaye ya damki makoshin Imhal da hannu daya ya daga shi sama tamkar ya daga sillan kara,sai gashi Imhal ya fara kakarin mutuwa,kawai sai garjejen katon yaci gaba da kyalkala dariyar mugunta sannan ya daga kansa sama yana duban Imhal yace,Kai yaro yau ka shigo kurkukun darul maut na birnin kisra,kurkukun da ba a fita sai dai gawa ta fita kuma gashi kayi rashin sa a ka shigo dakin dodon kowa a gidannan ZAUWADU,a dai dai wannan lokacine sauran fursunonin dake cikin sauran dakunan gidan suka kama lekowa dakin Zauwadu domin suga mai karar kwanan da aka kawo,ashe duk fursunan da aka kaishi dakin Zauwadu kawai so akeyi a kashe shi,Ba zato ba tsammani kawai sai Zauwadu yaji Imhal ya gabza masa mugun duka a fuska da kafarsa guda,Sabo da karfin dukan sai da Zauwadu yaga taurarin wuya bai san sanda ya dimauce ba ya saki wuyan Imhal ya fado kasa yana tari,koda Zauwadu ya shafa fuskarsa yaji jini sai ya fusata ainun ya juya bayansa inda Imhal ke kwance yana mai yin kururuwa kuma yakai masa mugun taku da kafa,cikin bakin zafin nama Imhal ya goce ya mirgina can gefe daya ya shammaci Zauwadu ya buga masa kafa akan marenansa,take Zauwadu ya sulale kasa

sumamme,koda ganin abinda ya faru sai gaba daya fursunonin gidan suka daina shewa da dariya suka kame kamar gumaka sabo da tsananin mamaki,Ba komai ne ya jefa fursunonin cikin tsananinb mamaki ba face ganin yadda aka samu jarumin da ya sumar da Zauwadu.Gaba daya fursunonin dake cikin kurkukun suna tsananin tsoron Zauwadu,kai ba ma fursunoninba su kansu dakarun dakaru dake tsaron fursunonin shakkarsa suke domin mutum goma basa iya ladaftar dashi sai dai ashirinb zuwa sama,duk da cewa dakarun kartine majiya karfin gaske wanda sai da aka zabo su,ko ya ya wani abu ya hada fursuna da Zauwadu to fa sai dai a sanya sunansa acikin matattu don ansan cewa Zauwadu ya kashe shi sabo da zaluncinsa,karfinsa da rashin imaninsa.Lokacin da Zauwadu ya farfado daga dogon suman da yayi yaga Imhal a zaune acan gefe daya kan shimfidarsa ya harde kafafu tamkarma ba fada sukayi ba sai ya fusata ainun musamman da ya waiga baya yaga gaba daya sauran fursunonin dake cikin sauran dakuna sun zubo idanu suna kallonsa,nan take zauwadu ya yunkura zai sake afkawa Imhal kawai sai gani yayi Imhal ya daka tsalle sama kamar dan biri ya dirga akan wuyansa ya shake shi,duk da tsananin karfi irin na Zauwadu sai gashi ya kasa kwacewa kuma idaninsa sunyi bulu-bulu sunyi jawur sai gashi yana dukushewa kasa yana kakarin mutuwa.Koda Imhal yaga Zauwadu na neman mutuwa sai ya sake shi ya zube kasa magashiyan yana numfashi sama-sama,take imhal ya nuna Zauwadu da dan yatsa ya dubeshi yace idan ka kara kawo miki wargi a karo na uku sai na kashe ka,Tun daga wannan rana Imhal ya zama shugaban fursunonin gidan gaba daya ya zamana cewa kowa yana shakkarsa ana yi masa ladabi da biyayya.A bangaren shugaban dakarun dake dake tsaron kurkukun kuwa,sai ya dauki kiyayyar duniya ya dora aka Imhal ya zamana cewa haka kawai sai yasa a kama Imhal a daureshi a tsaye da sarkoki ai ta dukansa da itatuwa har sai ya suma kamar gawa sai dai fursunoni su zo su dauke shi suyi masa magani,wani lokacin kuma ai ta gana masa bakar azaba iri-iri wacce duk fursunan da akayiwa ita sai ta zama sanadin ajalinsa amma sai gashi imhal yana jureta,duk da tsananin juriya irin ta Imhal sai da ya dinga ramewa yana yawan ramewa yana yawan rashin lafiya sabo da tsananin wahalar da yake sha,kai in ba don ma fursunonin suna matukar kaunarsa ba kuma suna gadin rayuwarsa ba,da tuni dakarun gidan sun kashe Imhal,komai rashin tausayin mutum idan yaga irin halin da imhal ya shiga sai ya tausaya masa,ba komai ne yasa fursunonin gidan suke matukar kaunar jarumi Imhal ba face zuwansa ya kawo adalci a tsakaninsu ya zamana cewa mai karfi ya daina zalunta mara karfi,a da,ko abinci fursuna ya karbo ya zauna zaici sai kaga wanda ya fishi karfi yazo ya kwace ya hada da nasa sai dai wancan ya kwana da yunwa,haka kuma akwai fursunoni masau mugayen dabi'u na yin luwadi ga wadan da sukafi karfi amma duk sai da Imhal ya hana yin wadannan mugayen abubuwa,Zauwadu da ya kasance babban makiyin Imhal sai da ya zamo babban amininsa kuma abokin shawararsa.

To jama'a ayi min afuwa idan na huta zan cigaba.

RIJIYA GABA DUBU1 CIGABA 10

Wata rana bayan an kama Imhal an kai shi wani daki na musamman inda ake yiwa fursunoni azaba,anyi masa dukan kawo wuka,sai aka dawo dashi dakin su aka warbar dashi a kasa jina-jina yana numfashi sama-sama kamar zai mutu,cikin dimaucewa Zauwadu ya shiga yi masa magani,da kyar ya samu ya tsayar da jinin da yake zuba a jikinsa,koda Imhal ya farfado ya dawo cikin hayyacinsa sai ya bude idanunsa dakyar ya dubi zauwadu yace Gobe idan na samu karfin jikina da cikin dare zan gudu daga cikin kurkukun nan,idan zaka iya bi na kazo mu gudu

tare mu tsira tare,koda jin wannan batu sai idanun Zauwadu suka zazzaro ya kamu da tsananin tsoro ya dubi Imhal cikin damuwa yace Ya kai abokina kayi sani cewa tunda aka gina kurkukun nan tsawon shekaru arba'in a baya ba'a taba samun fursunan da ya samu damar guduwa ba daga cikinsa,ta ya ya kake tsammanin kai zaka iya?ka dubi katangar gidannan wacce ta kasance mai tsananin tsawo da kauri,Ta ya ya zaka iya haurata ko fasata ba tare da anzo an kamaka ba?ka dubi yawan dakarun dake rangadi a harabar gidan nan a duk dare da rana,sannan ka dubi mugayen karnukan da suke gadin ko ina wadan da suka kasance manya tamkar kuraye sannan gashi sun samu da horo na musamman na iya kama mai laifi gami da tsananin karfin gudu gami da juriyar su.Idan baka sani ba to ka sani cewa gaba dayan kurkukun nan akan tsibiri yake,kuma shi tsibirin akan tsakiyar teku yake,idan ma ka samu nasarar fita daga cikin kurkukun nan ta yaya zaka iya ketare wannan teku har ka tsira da rayuwarka?Ai dabbobin dake cikin tekun nan ma kadai da sanyin teku sun isa su hallaka ka.Tabbas wannan kurkukun yaci sunansa DARULMAUT wato gidan mutuwa,duk fursunan da ya shigo gidan nan ya san cewa ya shigo gidan ajalinsa.Lokacin da Zauwadu yazo nan a zancen sa sai kawai yaji Imhal ya bushe da dariya al'amarin da yayi matukar bashi mamaki kenan ya kura masa idanu kawai ya kasa cewa komai,daga can sai Imkal ya nutsu ya dube shi yace Babu wani abu da bazai yiwu ba a doron kasa,kawai abinda nakeso dakai shine ka nemo mana kudade masu yawa wadan da zamu iya siyan ma'aikatan gidan nan,babu abinda kudi ba~ai iya yi ba.Koda jin wannn batu sai jikin ZauwadU yayi sanyi ya sunkui da kansa kas ya fada kogin tunani,Daga can sai ya dago kai(ya dubi Imhal yace Ya kai abokina ko na bika ko ban bika ba mutuwa zanyi acikin gidan nan don haKa gwara ma na bika din tunda babu wanda yasan abinda zai faru gobe,naga misali akan ha$uwa ta dakai,ban taba zaton za'a iya0samun furcunan da zai zo gidan nan ba har ya iya kainé kas sai gashi ma kai ka kaini kas har da sumar dani clhalil babu wan "DA" mai karfina kowa tsorona yake,dukkan fursunoni da ma'aikata amma sai gashh andawo andaina tsorona oai ake tsoro ana yi maka ladabi da biyayya.Ko da jin wannan batu sai farin ciki ya lullube Imhal ya rungume Zauwadu suka busHe da dariyar murna tare.Daca can sai Zauwadu ya janye jikinsa dag` cikin na Imhal ya dufe shi cikin nutsuwa a karo na biyu yace Ya kai abokina kayi sani cewa da dangari akan ci gari,a matsayina na fursuna da ya shekara ashirin da uku a cikin gidan nan nafi kowa sanin sirrin kurkukun nan acikin fursunoni domin babu wajda yayi dadewata kuma nafi kowa sanin irin ma'aikAtan da ya kamata mu hada kai dasu wajen samun nasarar wannan gagarumin aiki da m}keyi,Ina nufin dole ne mu zubo ma'aikatan da na tabbatar da cewa suna da kwadayin abun duniya,to amma inda íatsalar take shine ta yaya zamu iya samo kudaden da zamu biya ma'aikatan su`bamu hadin kai?Abu na biyu shine,har0yanzu bakq gaya min yadda zamu iya ketare tekun da ya zagaye gidannan bayan mun sami nasarar fita wajensa bc?Sa'afda Imhal ya ji wannan tambayoyi sai yayi murmushi yace abinda nakeso dakai shine ka bini!a sannu zamuyi komai dakm-daki da idanunka zaka ga amsoshin duk wadannan tambayoyin da kayi min yanzu.

tO JAMA'A AYIMIN AFUWA YANZU ZAKU DINGA JINA aKAI-AKAI ZAN DINGA POSTN DE WURI DON HAKA IDAN NA HUTA ZAN CIGABA!DAGA MAI SON NISHADANPAR DAKU COMBATANT33

RIJIYA GABA DUBU1 CIGABA 11

Abu na farko da nakeso mu farayi shine ina so mu hada baki da masu dafa abincin gidan nan,su zuba banju acikin abincin dakarun da suke gadin dakin shugaban dakarun gidan

nan,domin mu samu damar shiga mu balle akwatin da yake ajiye kudin hidimar gidannan aciki,na sani cewa akalla baza mu rasa dinare dubu dari ba acikin wannan akwatin wadannan kudade sun isa mu siye duk mutanen da mukeso suyi mana aiki,Zauwadu ya gyada kai yace tabbas zasu ishe mu,amma ta yaya zamu samu amincewar ma'aikatan da suke dafa abinci su zuba banju acikin abincin?Imhal yace baza mu iya yin wannan aiki mu biyu kacal ba,dole sai mun nemi hadin kan yan'uwan mu fursunoni akalla mutum goma,cikin tsananin firgici Zauwadu yace idan muka gayyato mutane cikin wannan aiki namu za a iya samun rashin sirri a ciki,acikin mu za a iya samun munafikin da zai zagaye ya tona asirin mu,Imhal ya gyada kai yace ai ba kowa zamu tabo ba sai wanda mukasan ya gari da zaman gidannan kuma yana da taurin rai gami da sai da rai,haka kuma duk wanda ya shigo cikinmu zamu gaya masa idan har ya tona mana asiri aka kamamu hukuncin kisa ne akan sa,koda jin wannan batu sai Zauwadu yayi murmushi yace hakika kwakwalwarka tana aiki sosai to idan muka samu mataimakan ta yaya zamu samu hadin kan masu dafa abincin?Imhal ya sake murmushi a karo na biyu yace ka sani cewa masu dafa abincinnan fursunoni ne yan'uwanmu dole ne mu firgita su mu kashe daya daga cikinsu  a gaban idanunsu sannan mu umarce su da abinda muke bukata  kuma mu gargadesu cewa duk wanda  ya tona asirinmu acikin su shima mutuwa zai yi,koda jin haka sai Zauwadu yayi dariyar farin ciki yace tabbas indai mukayi haka komai zai tafi dai-dai to amma fa kasani idan muka debo wadannan kudaden acikin sa'a daya asirinmu zai tonu don a sannan ne shugaban dakarun zai dawo,koda jin haka sai Imhal yayi tsaki ya mike tsaye zumbur a fusace ya dakawa ALZauwadu tsawa yace kada ka sake yimin tambayar komai har sai bayan mu samu nasararr fita daga gidannan.Gama fadin haka ke da wuya sai suka ji an kada kararrawar zuwa cin abinci nan take dakaru suka fara bude kofofin dakunan fursunonin,ana bude dakin su Imhal sai suka wuce da sauri suka zama akan gaba suka riga kowa zuwa inda masu dafa abinci suke suka shige har cikin dakin girkin ba tare da dakaru sunga lokacin da suka shiga ba,suna shiga suka iske masu dafa abincin akan aikinsu kawai sai Zauwadu ya kama kan daya daga cikin su ya murde ya yar da gawrsa a kasa,cikin tsananin tsoro sauran ma'aikatan suka zube a kasa suna rokon su ayi musu rai kawai sai Imhal ya dube su yace idan kuna so ku tsira da rayuwarku ayau ku zuba banju acikin abincin da za a kaiwa masu gadin shugaban dakarun gidannan idan kuma kuka gayawa wani wannan sirrin duk sai kun mutu lallai kuyi wannan aikin cikin dakiku kadan,koda gama fadin haka sai Imhal da Zauwadu suka fice daga cikin dakin suna fita kuwa suka yi arba da wani babban badakare akayi kallon-kallo nan take jikin badakaren ya bashi cewar da akwai abinda suke shiryawa.

TO JAMA'A ANAN NAZO KARSHEN LITTAFI NA DAYA IDAN NA HUTA ZAN CIGABA DA LITTAFI NA BIYU DAGA MAI SON NISHADANTAR DAKU COMBATANT33